# Wanda ke kan abin hawa shi ke sallama ga mai tafiya, mai tafiya kuma yana sallama ga wanda ke zaune, kadan kuma (suna sallama) ga masu yawa

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce : Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Wanda ke kan abin hawa shi ke sallama ga mai tafiya, mai tafiya kuma yana sallama ga wanda ke zaune, kadan kuma (suna sallama) ga masu yawa". Ga Bukhari: "Karami yana sallama ga babba, mai tafiya ga na zaune, kadan ga mai yawa".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana shiryarwa ga ladabin yin gaisuwar Musulunci tsakanin mutane "Aminci ya tabbata agare ku da rahamar Allah da albarkarsa", Sai karami ya yi sallama ga babba, wanda ke kan abin hawa ga mai tafiya a kasa, mai tafiya a kasa ga wanda ke zaune, adadi kadan ga adadi mai yawa.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee